# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tsabta
## Kashi na shida: Wanke hannaye


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Nkoji C. Muhoho |
| Wanda ya tace: | Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Kabir Isa Jikamshi |


**’Yan wasa:**

| | |
|---|---|
| Sama’ila: | ɗan shekara 17 |
| Bilkisu: | ’yar shekara 40 |
| Mariya: | ’yar shekara 43 |
| Hadiza: | ’yar shekara 15 |
| Adamu: | ɗan shekara 36 |

Ɗalibai maza

**MAI GABATARWA:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wasan kwaikwayonmu na shida cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" inda muke kawo muku ƙarin haske game da batutuwan kula da lafiya da kuma yaƙi da cutar gudawa.

A shirin da ya gabata mun tsaya a inda Sama'ila, da 'yan gidansu da kuma abokan arziki suka fahimci cewar ita ma tsutsar ciki na ɗaya daga cikin hanyoyin da suka zama ruwan dare waɗanda za su iya haddasa kamuwa da cutar gudawa. Sun kuma shaida hanyoyi masu yawa da za a iya gurɓata ruwan sha. A cikin shirin na yau, za ku ji yadda mutanen wannan ƙauye za su fara koyon ingantattun hanyoyi ne kan yadda za su riƙa sarrafa ruwan da suke amfani da shi. Sai ku kasance da mu a yau domin ku sha bayani.

**Fitowa ta 1: A gidan Bilkisu**

Mariya, Bilkisu, Hadiza, Sama'ila

| | |
|---|---|
| **MARIYA** | Bilkisu, wata irin baƙar yunwa nake ji, kamar na haɗiye doki. |
| **BILKISU** | Ba su da dawakai a nan, Mariya maƙwabciyata. Mai yiwuwa dai ko jaki. |
| **MARIYA** | *Ha ha ha.* Na san kin san abin da nake nufi. Ba ni wancan tumaturin in sha, kafin ki gama dafa abinci. … Allah mai iko! Yaya abin yake ɗaukar lokaci haka? Sama'ila, miƙo mini tumaturi nan daga cikin waccan jakar. |
| **SAMAILA** | Kina son wanda ya nuna ne sosai, ko kuma wanda bai nuna sosai ba? |
| **BILKISU** | Ka dai ba ta tumaturin kawai! |
| **HADIZA** | Amma fa sai mun wanke shi tukuna. |
| **MARIYA** | Hadiza, kina zaune kusa da jakar tumaturi, kuma ina jin yunwa. A saboda me za a riƙa wasa da ƙwaƙwalwata a kan |

| | |
|---|---|
| | tumaturi guda ɗaya kawai? Ki kasance 'ya ta gari, ki ba ni tumaturi kawai. |
| **SAMA'ILA** | Ya kamata mu wanke shi, kuma cikin minti ɗaya zan yi hakan. |
| **MARIYA** | Miƙo mini wancan tumaturin! |
| **HADIZA** | Amma fa ya zama wajibi mu wanke shi tukuna! |
| **MARIYA** | Don Allah, ki miƙo mini tumaturin nan, haba! |
| **BILKISU** | Don Allah, wani ya ba ta tumaturin nan mana! |
| **SAMAILA** | Anti Mariya, ki tuna abin da na yi wa lambunki lokacin da na yi fama da cutar gudawa. Kuma kina son ki ci dukkan wannan ƙazanta daga cikin wannan tumaturin da ba a wanke ba? |
| **MARIYA** | Haba! Kai, me kake jira? Wanke, ka kuma busar mini da tumaturin nan yanzu! Ko kana so ka ba ni shi ne ba tare da an wanke ba? Hakan zai sa dukkan wannan gubar ta shiga cikin cikina. Maza ka wanke ka miƙo mini shi don Allah! |

**Fitowa ta 2: A gidan Bilkisu**

Bilkisu, Mariya, Hadiza, Sama'ila

| | |
|---|---|
| **BILKISU** | Sama'ila, don Allah ka miƙa wa Mariya wannan abincin. |
| **MARIYA** | Haba Bilkisu, har yanzu kina da sauran abinci a cikin tukunyarki? Ko za ki ɗan ƙara mini? Na faɗa miki cewa ina jin wata irin masifaffiyar yunwa ne. |
| **BILKISU** | To, Mariya. Kina faɗin gaskiya ne. |
| **SAMA'ILA** | Ga abincinki. |
| **MARIYA** | Yauwa! Na gode Sama'ila. Kin yi gaskiya, Bilkisu. Idan mutum yana jin yunwa, don me zai ɓoye? Na sha yunwa a |

| | |
|---|---|
| | duk tsawon rana. Ki gafarce ni idan ban jira ki ba, don yunwa nake ji sosai. Zan saka hannuwana kawai in fara cin abinci. |
| **SAMA'ILA** | Dakata, dakata! |
| **HADIZA** | Dakata, Mama! |
| **BILKISU** | Yanzu kuma, sai me? Yaran kawai, wai mene ne ya shiga kawunanku ne? Da farko kun nemi ku hana ta tumaturi, yanzu kuma ba kwa son ta sanya hannunta a cikin abinci. |
| **SAMA'ILA** | Ba dai hannuwanta ba, sai dai yatsunta, Mama! |
| **MARIYA** | Bari ku ji. Zan ci abincina ta yadda nake so. |
| **SAMA'ILA** | Ba na son ki kamu da rashin lafiya kamar yadda na sha fama. |
| **HADIZA** | Don Allah, Mama, kar ki bari wani abu maras daɗi ya faru da ke, kamar yadda ya faru da jinjira Fati. Don Allah, Mamana, ba na so ki mutu. |
| **BILKISU** | Mariya, yanzu dubi abin da kika yi wa 'yarki. Ga shi kin kusa sanya ta hawaye. Wanke hannuwanki! |
| **MARIYA** | Saboda me, sai ni kaɗai? Bayan kuma, ba ni kaɗai ba ce nake tattaɓa abubuwan da ke nan wurin. Ko kuna nufin, ni ce kaɗai ƙazama? |
| **HADIZA** | A'a Mama, ba batun ƙazanta ba ne. Kwayoyin cutar yaɗuwa suke a ko'ina: a ƙasa, a hannuwanmu da muke gaisawa da su, a kan abubuwan da muke ɗauka. A taƙaice dai, kusan ko'ina. Ko ba haka ba ne, Sama'ila? |
| **SAMA'ILA** | Haka ne. Kin yi tunani game da abubuwan da na taɓa, ko wuraren da na ajiye tufafina lokacin da nake rashin lafiya? |
| **MARIYA** | Idan na tuna hakan, nakan ji kamar in fice daga gidan nan, in ƙi dawowa. |
| **BILKISU** | Sama'ila, kana ƙoƙarin tsorata aminiyata ce ko? |

**HADIZA** A'a, ba batun tsorata kowa ba ne. Muna dai matuƙar ƙaunarku ne kawai, kuma muna son ku kasance cikin ƙoshin lafiya.

**BILKISU** Ku ci abincinku mana! Yana ƙara yin sanyi.

**SAMA'ILA** Hadiza, kawo mana waccan robar ruwan da sabulu, domin mu wanke hannuwanmu.

**MAI BA DA LABARI:**
Kun ji fa, masu saurarenmu, ga dukan alamu manya ne ya kamata su samu ƙarin ilimi sosai fiye da yara game da hanyoyin yin rigakafin kamuwa da cutar gudawa. Shakka babu, Sama'ila da Hadiza sun koyi darasi bayan da cutar gudawa ta ziyarci gidan Bilkisu, har ta yi sanadiyyar mutuwar jinjira Fati. Bayan cin abincin rana, waɗannan matasa sun yi wani tattaki zuwa cikin gari.

**Fitowa ta 3: A wata ƙaramar hanya**
Hadiza, Sama'ila

**HADIZA**
*Ku wanke hannuwanku,*
*ku wanke hannuwanku,*
*ku wanke hannuwanku,*
*a yayin cin abinci.*
*Malallatan mutane*
*ba sa wanke hannu*
*a yayin cin abinci,*
*da zarar sun fito*
*daga banɗaki a kullum.*

Ya yi! Yanzu, sai ka kwaikwaye ni, kuma ka yi waƙar kamar yadda take.

**SAMA'ILA**
*Ku wanke hannuwanku,*
*ku wanke hannuwanku.*

*Malallatan mutane…*

**HADIZA** A'a, a'a! Tsaya, tsaya! Gaskiya, ba ka iya baitun waƙar ba, kwata-kwata.

**SAMA'ILA** Aƙalla dai na iya faɗin kalmomin daidai! Na yi alƙawari zan samu baitun waƙar daidai. Amma nan gaba, ba yanzu ba.

**HADIZA** Ba zan saurara maka ba, Sama'ila, har sai ka iya rera waƙar nan kamar yadda take.

**SAMA'ILA** To, shi ke nan, na yi alƙawarin zan koya. Yanzu kuma, ko za mu yi 'yar tsere ya zuwa waccan bishiyar?

**HADIZA** Bismillah. To, ka shirya? … A'a'a'a, gaskiya ban yarda ba, Sama'ila! Ka dawo! Gaskiya ban yarda ba!

**SAMA'ILA** Ina son in nuna cewa ƙarfina ya sake dawowa. Na zaƙu a fara gasar guje-guje na gaba a makaranta!

**HADIZA** Muna fatan ka ci gasar!

**SAMA'ILA** Fata? Kika ce "fata"? Zo nan, sai na koya miki hankali!

**HADIZA** Wallahi, ka daina haka Sama'ila, ka bari! Ba na so, ka bari, na tuba! ...

**SAMA'ILA** To shi ke nan, zan daina.

**HADIZA** Na ji! Amma Sama'ila, ina tunanin cewa za mu riƙa koyar da wannan waƙar ga dukan ɗaliban makaranta. Kuma za ta riƙa taimaka musu cewa a ko da yaushe su riƙa wanke hannuwansu. Ko yaya ka gani?

**SAMA'ILA** Gaskiya ne, kuma kin ga ta haka, ba za su kamu da cutar gudawa ba, kamar yadda na yi fama da ita.

**HADIZA** Haka ne. Idan suka riƙa wanke hannuwansu a kai-a kai, ba za su riƙa yin rashin lafiya ba, ballantana su kasa zuwa makaranta kamar yadda ka yi. Ka gane?

**SAMA'ILA** Ko su mutu ba, kamar yadda ƙanwata Fati ta yi.

**HADIZA** E, dole mu koya musu! Bari ma yi wa malama magana, gobe.

| | |
|---|---|
| **SAMA'ILA** | E! Bari mu… yanzu kuma zan yi galaba a kanki idan muka yi tsere ya zuwa ƙarshen hanya. … A'a, Hadiza, ban yarda ba wallahi! Ki dawo baya! Yaya za ki tafi ban shirya ba? Gaskiya kin yi magudi, ban yarda ba! Sam ba ki galaba a kaina ba. Kawai ki dawo baya! |

**MAI BA DA LABARI:**
Shakka babu Sama'ila da Hadiza yaran kirki ne. A matsayinsa na wanda ya yi nisan kwana, Sama'ila zai yi amfani da halin da ya samu kansa, domin ya sanar da sauran matasa game da cutar gudawa. Da shi da Hadiza za su iya wannan aiki ne ta wasu dabaru don su jawo hankalin matasan, misali ta yin amfani da waƙa.

**Fitowa ta 4: A gidan Bilkisu**
Adamu, Bilkisu, Sama'ila, Hadiza

| | |
|---|---|
| **ADAMU** | Na bari ayyukan kula da lafiya na al'ummar gari sun janye hankalina, amma akwai abin da ya fi muhimmancin lafiyar 'yan'uwanka? |
| **BILKISU** | Ah, Malam Adamu, muna godiya ƙwarai. |
| **ADAMU** | Sama'ila, yaya makarantar? |
| **SAMA'ILA** | Lafiya ƙalau, Kawu Adamu, amma akwai tarin aikin da aka yi ba na nan, wanda ya kamata in yi. |
| **ADAMU** | Tsawon wane lokaci ne ba ka je makarantar ba? Ya kai makwanni biyu? |
| **HADIZA** | Ya yi asarar kwana sha bakwai ne cif-cif. |
| **BILKISU** | Hadiza, ya kamata ki ƙyale abokinki ya ba da amsa da kansa. |
| **SAMA'ILA** | Kusan makwanni uku, Kawu. Amma… uhmmm… amma…. |

**ADAMU** Akwai wata matsala ke nan.

**SAMA'ILA** Yanzu ganin cewa, na taɓa yin fama da cutar gudawa, kuma na san yadda na same ta, ina cikin damuwa saboda sauran ɗalibai za su riƙa fuskantar wannan cuta a kai-a kai.

**ADAMU** Saboda me ka yi wannan tunanin?

**SAMA'ILA** Ba sa wanke hannuwansu, kuma… kuma… Kawu, banɗakunanmu suna…

**HADIZA** Banɗakunanmu suna da datti, kuma wasu ɗaliban ba sa wanke hannunsu yayin da suka yi amfani da su.

**ADAMU** Zan iya zuwa makarantarku na yi muku jawabi. Wannan shi ma wani ɓangare ne na aikina a matsayina na ma'aikacin kyautata jin daɗin jama'ar garin nan.

**HADIZA** Kai! Ya yi kyau, ya yi daidai!

**SAMA'ILA** Kawu Adamu, don Allah ka zo ka taimake mu!

**MAI BA DA LABARI:**
Wannan ya nunar da cewar ɗaukar nauyin koyar da tabi'u na ƙwarai domin kula da lafiya ba zai tsaya ba ne kawai a gidajen yara. Ya zama wajibi su tabbatar da cewa abokansu a makaranta, su ma suna da ilimi kwatankwacin wanda suke sani game da kiwon lafiya. Sai ku biyo mu domin jin yadda za ta kasance a cikin ajin su Sama'ila.

**Fitowa ta 5: A makarantar sakandare**
Adamu, Bilkisu, Sama'ila

**SAMA'ILA** Barkanku da safiya, abokaina 'yan makaranta. … Muna godiya ga Malama Grace da ta ba ni damar kawo kawuna Uncle Adamu, domin ya ilimantar da mu game da kula da lafiyarmu. Ina farin cikin gabatar muku da kawuna, wanda

shi jami'in kiwon lafiyar jama'a ne. … Ina kuma murnar gabatar muku da makwabciyarmu Hadiza, wadda ita ma ɗaliba ce a makarantar 'yammata da ke kusa da wannan makarantar. Yawancinku, kun san ta.

**ADAMU** Ina godiya ƙwarai ga Malama Grace da ɗana Sama'ila da abokiyarsa Hadiza, saboda gayyatar da kuka yi mini. Kamar yadda kuka sani, Sama'ila ya shafe kusan makwanni uku bai zo makaranta ba. Ya yi fama da cutar gudawa. A saboda wannan jinya da ya yi, mun koyi abubuwa masu yawa. Don haka muke son sanar da ku abin da muka ƙaru da shi. Da farko dai, Sama'ila da Hadiza suna da wata waƙar da za su koya muku. Wannan waƙa za ta bada ƙarin haske game da batun wanke hannuwanmu. Sai a karkaɗe kunnuwa, domin ji daga bakin Sama'ila da Hadiza.

**SAMA'ILA da HADIZA**

*Mu wanke hannuwanmu,*
*mu wanke hannuwanmu,*
*mu wanke hannuwanmu,*
*a yayin cin abinci.*
*Malallatan mutane*
*ba sa wanke hannu*
*a yayin cin abinci*
*da bayan sun fito*
*daga banɗaki a kullum.*

**ADAMU** Yauwa! Kai! Da kyau ƙwarai! Mu sake tafa musu. Sama'ila da Hadiza, ina son ku koya wa dukan ɗalibai wannan waƙar.

**SAMA'ILA da HADIZA** To, Uncle Adamu.

**ADAMU** Na yi murna cewa, kuna ɗokin lamarin. A duk lokacin da kuka rera wannan waƙar za ta tunatar da ku cewa, dole ku riƙa wanke hannuwanku. Bari mu yi waƙar!

**ƊALIBAI** *Mu wanke hannuwanmu,*

*mu wanke hannuwanmu,*
*mu wanke hannuwanmu*
*a yayin cin abinci.*
*Malallatan mutane*
*ba sa wanke hannu*
*a yayin cin abinci*
*da bayan sun fito*
*daga banɗaki a kullum.*

**MAI GABATARWA:**

Masu saurarenmu, a yau kuma a nan za mu dasa aya a cikin shirin. Sai kuma a mako na gaba inda za ku sake sauraron wani sabon shiri. Amma za ku iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe, domin sake sauraron wannan shiri.